# Kwayoyin Maganin Tazaran Haihuwa Na Gaggawa



## CHIKAKKEN BAYANI:

- Amfani da kwayoyin tazarar haihuwa na gaggawa na da ingaci ta hanyar bada kariya daga daukar ciki bayan jima'i
- Kwayoyin tazarar haihuwa na gaggawa na daga cikin ire iren kwayoyin tazarar haihuwa ta musamma
- Shan kwayar tazarar haihuwa na gaggawa a cikin awa dari da ashirin bayan jima'I na bada kariya daga daukar ciki.
- A sha kwayar da gaggawa bayan jima'i. An fi samun biyan bukata idan aka yi amfani da kwayar cikin gaggawa bayan jima'i, harkazalika Jinkirta shan kwayar bayan jima'I na rage ingancin ta.

## INGANCIN KWAYOYIN TAZARAR HAIHUWA NA GAGGAWA WURIN KARIYA DAGA DAUKAR CIKI:

- Idan an sha maganin a cikin awa dari da ashirin bayan jima'i ba tare da kariya ba, kashi saba'in da biyar (75%) daga cikin catsa'in (95%) baza su samu juna biyu ba.

## YADDA KWAYOYIN SUKE AIKI:

- Maganin na zuwa a cikin kunshi mai kwayoyi biyu ko mai kwaya daya
- A karanta cikakkun bayanen dokokin shan maganin kafin a sha
- Sinadarin da ke cikin kwayoyin yana hana maniyin na Miji haduwa da kwan na mace
- Bayan haka wannan sinadarin ya na hana saukar kwan mace

## INGANTATTUN BAYANAI GAME DA KWAYOYIN:

- Ana amfani da kwayoyin nan ne cikin gaggawa kadai bayan jima'I, ba kwayoyin sha na amfanin yau da kullum ba ce.
- Bai dace a sha kwayoyin nan fiye da so biyu a wata ba
- Akwai Karin hadarin gazawar maganin idan ana sha akai-akai yau da kullum.
- Basa iya karya ko lallata juna biyu (ciki)
- Kwayoyin na bada kariyar duakar ciki idan an yi amfani da shi bayan yan kwanaki cikin awa dari da asirin da jima'I ya faru.
- Kwayoyin basa bada kariya daga kamuwa da ciwon sida ko chututtukan da ake dauka wurin jima'i.

## FA'IDAR AMFANI DA KWAYOYIN TAZARAR HAIHUWA NA GAGGAWA:

- Baya kawo matsala ga akasarin mata komin matsayin halin lafiyar su da shekarun su
- Ana samun kwayoyin a wuraren kiwon lafiya da shagunan magunguna masu izini
- Amfani da kwayoyin na kare cikin da ba a shirya wa ba harkazalika ta na rage bukatar zubar da ciki
- Ba su da hadari ga juna biyu (ciki)

## DOMIN KARIN BAYANAI GA KWAYOYIN TAZARAR HAIHUWA NA GAGGAWA:

- A karanta takarda mai dauke da cikakken bayani
- A ziyaci kwararrun ma'aikatan kiwon lafiya

**A KULA:**
**A maimata kwayoyin idan an yi amai bayan awa biyu da sha**

Get it together
KNOW. TALK. GO.

NURHI 2
NIGERIAN URBAN REPRODUCTIVE HEALTH INITIATIVE

